WASAN ' YAR TSANA A MATSAYIN TUBALIN GINA TARBIYYA A KASAR HAUSA

Muhammad Tahir Rabiu

Tsakure

Tarbiyya hali ne na ɗan Adam wadda takan yi tasiri a kan rayuwar mutum. Ana iya fahimtar irin wannan halin tarbiyya a cikin wasan 'yar tsana. Domin wasan yana ƙunshe da bakandamen jigo, da sauran jigogi waɗanda suke sakayau, ba su tare da tarbiyya kai tsaye. Domin haka ne wannan muƙala take ƙoƙarin leƙo tarbiyya a matsayin tubulin gina al'umma a cikin wasan 'yar tsana. Tarbiyya hanta ce da jini a rayuwar al'umma, da ita ne al'umma ke iya cim ma burinta na yau da kullum. A kan wannan turba ce muƙalar ta fara da gabatarwa wadda ta ƙunshi bayani a kan tarbiyya, da kuma dangoginta masu nasaba da tarbiyya. Sannan muƙalar ta shiga tsokaci kan wasu ɓangarori na wasan 'yar tsana wanda tarbiyya ta malala a ciki.

1.0 Gabatarwa :

Maƙasudin wannan muƙala shi ne ta tabbatar da cewa, wasan 'yar tsana wani tsani ne da ake iya hawa wajen gina tarbiyya a ƙasar Hausa. Wasan 'yar tsana wasa ne wanda yake bakandame, domin ya ƙunshi rayuwar 'ya mace tun daga tsumman goyo har zuwa aure. Domin tarbiyya ga Hausawa tana farawa ne tun daga renon ciki har zuwa mutuwa.

Hausawa na ɗaukar tarbiyya wani babban masaki wanda yake kai al'umma tudun-muntsira a rayuwa, kuma da ita ne al'umma ke zama abin alfahari da kwatance domin a yi koyi da ita.

Tarbiyya harka ce wadda kusan kowa a cikin al'umma yake ba da tasa gudummuwa gwargwadon matsayinsa da kuma yanayin shekaru ko kuma muƙami da dangantakar mutum. Da haka ne ake iya cewa al'umma na iya zama jami'an tarbiyya a cikin al'ummarsu. Sai dai haka ba yana nufi tarbiyya an barta kara zube ba ne, akwai tsari dangane da yadda kowa ke iya ba da ta shi gudunmawar, tun daga iyaye har zuwa sauran al'umma. (Umar, 1987 : sh 3-6)

Shi kuwa wasan 'yar tsana wasa ne da kullum yake leƙa wa, ya gano matsalolin da suke faruwa a tsakanin al'ummarsa, ko suke dabaibaye da

al'amuran rayuwa na wannan al'umma domin samun damar yin tsokaci. Domin harkoki irin na auratayya da na maƙwabtaka da tarbiyyar yara duk suna da babban tasirin a wasan.

2. 0 Ma'anar Wasan Kwaikwayo

Masana da manazarta da ɗalibai sun tofa albarkacin bakinsu, dangane da abin da ake nufi da wasan kwaikwayo. Domin akwai wasa da kuma wasan kwaikwayo kamar yadda Malumfashi (1989), da Ahmad, (1985) da Sambo, (1990) sun ba da ma'ana ta wasan kwaikwayo kusan abu ɗaya sai dai ɗan bambancin da ba a rasa ba a tsakanin masanan.

Shi kuwa Yahaya, (1978) ya bayyana cewa ai da jin sunansa, wasan kwaiwayo ya bayyana kansa, watau akwai alamun wasa, abin da yake raha da kuma alamun kwaikwayo, aikata wani abu don kwatanta yadda ake yinsa, domin wani ya gani ya gane kyan abin ko muninsa. (Yahaya,1978: sh 4-6)

Waɗannan bayanai suna nuna mana cewa wasa yana da danganta da duk wani abu ke nan wanda ba gaskiya ba, sannan kuma da nufin koyan wani abu ko ganin wani abu, domin al'umma su gyara ko kuma su yi wani aiki wanda ya danganci al'amuran rayuwarsu na yau da kullum. Saboda haka wasan kwaikwayo musamman wasan, wanda yake kusan lulluɓe da tarbiyya tun daga farko har zuwa ƙarshe.

Saboda haka idan aka ce wasa wani abu ne da ake yi don nishaɗi ko annashuwa, a aikace ko a magance wanda yake iya ɗaukar sifofi na sauya kama, domin isar da wani saƙo ko hannunka mai sanda ga al'umma. (Malumfashi, 1985: sh 3-6)

Wasu na ganin cewa wasan kwaikwayo yana ɗauke ne, da wata fasaha wadda ke samar da nishaɗi da annashuwa ga masu kallo ko sauraro da rayuwar al'umma ((Malumfashi, 1987: sh . 6)

Saboda haka kusan a iya cewa waɗannan ma'anoni sun taimaka wajen fito da ma'ana ta wasan kwaikwayo a fannin ilimi na musamman, ko da yake a iya fito da wata ma'ana wadda za ta taimaka wajen haɗe tama da ƙarfe, domin samun dacewa da abin da masana suka faɗa. ke nan a iya cewa wasan kwaikwayo yana iya ɗaukar duk wani abu da ya danganci wasa da nufin kwaikwayon abin da wata al'umma ya dace ta aikata ko kuma ta gyara domin ci gaban al'ummarta wajen saita tunani da sauya tunani.

3. 0 Wasan 'Yar Tsana

Wasan 'yar tsana wasa ne da ya ƙunshi yara ƙana, wanda suke aiwatar da shi domin nishaɗi a tsakaninsu da sauran yara. Tun asali Hausawa suna da wasan 'yar tsana ko yar ƙashi, wanda suka ƙirƙiro shi da kansu, domin nishaɗi da nusarwa. Saboda haka, wasan 'yar tsana ya ginu a dalilin gargajiya da al'adar rayuwar Hausawa. Da haka ne wasan ya kusan zama ko'ina an san shi ko an taɓa yi a lokacin ana yara.

Har ila yau, wasan 'yar tsana yara mata ne suke aiwatar da shi, don kuwa su 'yan matan za su sami ƙashi su shirya shi kamar wata yarinya. *Wannan ƙashin za a yi ta reno tun daga haihuwa ya zuwa lokacin da za a yi 'mata' aure. A wannan lokacin har goro da deman minti ake rabawa domin gayyata ga sauran 'yan mata 'yan uwanta.* A irin wannan wasan ana kwaikwayon yadda ake gudanar da halin rayuwa. A lokacin za a reni yarinyar, a koya mata tarbiyya da duk wasu halayen kirki da ake so ta koya. (Ahmad, 1990: sh-2-6)

Kamar yadda bayani ya nuna cewa yara mata ke aiwatar da wasan 'yar tsana, da nufin koyan halin rayuwa da tarbiyya da nishaɗi. wannan ya nuna ke nan idan har za a koyi tarbiyya tun daga ƙuruciyar 'ya mace, ya bayyana an fara samun tubulin gina tarbiyyar wannan yarinyar tun daga wasan 'yar tsana.

Bikin 'yar tsana yara mata su ne suke yin wasan, yarinya, idan ta mallaki 'yar tsana, sai ta riƙa yi mata renon yarinya ta gaske, ta dinga kwaikwayon ciyar da ita, tana yi mata wanka. Idan ta girma, ta yi mata ƙunshi, da ado na tufafi wanda teloli suka ɗinka da ƙyallaye. A kwana a tashi sai ta ce ita yarinyarta ta isa aure, sai ta raba wa ƙawayenta goro da alewa, ta gaya musu ranar biki. Sai ta tanadi ƙananan kwanuka da tasoshi, har ma da ɗan gado, matasan kai, da kumbuna ko kobot. Su kuma ƙawaye su zo ranar kamu, su suffanta duk abubuwan da manya suke yi na bukukuwan aure tun daga ranar kamu har su ƙunshi da tarewa. Sukan kawo kuɗin gudummawa wurin uwar 'ya. (Yahaya, 1987 : sh-7)

Saboda haka wasan 'yar tsana wasa ne, da ya ƙunshi ƙananan yara mata, wanda yake da lafazi kusan nau'i biyu, na manya da kuma lafazin yara 'yan wasan. Akan sami kan rake ko ƙashin ƙafar dabba (akuya ko tunkiya da sauransu), sai a mai da shi kamar 'ya ta gaske, za a raine ta da kuma ba ta tarbiyya kamar yadda yaran suka gani a wajen iyayensu, za a kai ga yaye da kuma koya mata sauran abubuwan kamar sanya tufafi da kwalliya da kuma iya magana yadda ya dace, har zuwa lokacin aure. Daga nan ne za a raba goro a gayyaci maƙwabta yara su zo domin a aiwatar da sha'anin biki, har zuwa gidan miji kamar tare wa da yi mata faɗa, ta yadda za ta zauna da miji lafiya da kuma sauran makwabta.

4. 0 Tubalin Gina Tarbiyya

4. 1 Harshen:

Wasan 'yar tsana harshe ne, wanda yake mai tafiya da yadda manya suke a wannan lokaci, wanda ya ƙunshi iyaye da kuma mai gida, lafazinsu na iyaye, duk da karin murya irin na manya, wani lokaci za a ji mai gida yana yi ma iyalinsa faɗa, musamman idan sun yi wani abu ba dai-dai ba, wani lokaci kuma harshen wasan yana magana kwatankwacin yadda zama yake a tsakanin iyaye da 'ya'yansu, sau da yawa za a fahimci yara sun raba gidan wasan 'yar tsana zuwa gida biyu, da gidan da ake aiwatar da wasan ya haɗa da uwa da 'ya da mai gida, sannan makwabta waɗanda su ne ake gayyata wajen bikin 'yar tsana. Haka kuma lafazin wasan yana haɗa lafazin yara da kuma na manya dangane da yadda wasan yake tafiya, har lokacin da za a aurar da 'yar tsana.

4. 2 Haihuwa:

Haihuwa wata hanya ce ta samun zuriya mai kyau, a wasan 'yar tsana yara kan fara rainon cikin haihuwa tun daga lokacin da wasan ya fara kankama. Sai su fara nuna wa mai ciki ga yadda za ta yi wajen kula da abin da ke cikin ta, ta nuna shan waɗansu jiƙe-jiƙe a wasance, da kuma faɗakar da ita nauyin da ke kanta na kula da cikin kafin tahaihu.

4. 3 Reno:

Uwa a wasan 'yar tsana tana fara renon yarinyarta ne tun daga lokacin da ta haifi yarinyar. Wani lokaci ma uwar kan yi ƙoƙarin ba yarinyar abinci da koya zama da rarrafe da sauran zantukan yau da kullum, duk haka yana faruwa ne a yayin da ake cikin gudanar da wasa.

4. 4 Yaye:

An shiga mataki na gaba ke nan wajen gina tarbiyya a wasan, daga wannan lokai ne ake fara koya wa yarinyar sanya kaya ko tufafi. Da kuma nuna wa 'yar yadda ake yin tsarki da wasu hidindimu, kamar fahimtar jama'ar gida tun daga ita kanta uwa da kuma sauran maƙwabta, sannan a wannan lokaci ne za a fara nuna mata wasu halaye kamar ladabi da biyayya, aka kuma fara nuna mata ado kamar yi mata ƙunshi da tufafi da sauransu.

4. 5 Budurci:

A lokacin da yarinya ta kai budurwa, a wasan 'yar tsana sai ka ga ana shirye-shiryen koya wa yarinya wasu halaye na alkunya da juriya da kuma nuna karamci da sauran kyawawan ɗabi'u. sannan ana koya mata guje wa munanan halaye, da kuma yadda ake zama da jama'a. haka kuma a wannan lokacin ne ake fara shirya biki, za a tanaji 'yan kwanoni da tasoshi da gado. Daga nan sai a raba goron gayya zuwa ga ƙawaye, har zuwa lokacin da za a kai ga biki, za a yi biki kamar yadda manya ke yi wadanda suka haɗa da sa lallae da tarewa da sauran al'amuran aure.

5. 0 Kammalawa:

Wasan 'yar tsana wasa ne wanda yake ɗauke da dunbin tarbiyya ga al'ummar Hausawa. Domin wasan ya sama da nuna yadda ake fara tarbiyya tun daga harshen wasan, wanda shi ne yake kusan ɗauke da wasu sassan tarbiyya, sannan wasan ya tattake wuri da yin nuni da koyo da koyar wa musamman tun daga tsumman goyo har zuwa aure. Wasan 'yar tsana bakandamen wasan ne wanda yake nuna wa 'ya mace yadda ake tarbiyya, idan ta kai yanayin budurci. Haka kuma wasan yana tanadar kusan duk wani nau'in yanayi na tarbiyya yadda ake tusa ta ga 'yar tsana domin masu sauraro ko masu kallo. Saboda haka wasan 'yar tsana hanya ce da za a iya amfani da ita wajen ɗora al'umma akan turba mai kyau.